# HUJJOJI KAN MAULUDI

<"xml encoding="UTF-8?>

HUJJOJIN YIN MAULUDI KASHI NA DAYA

Da sunan Allah, Mai Rahama, Mai Jin  ai, Tsira da Amincin Allah su Tabbata, ga Manzo da .Alayensa, Tsarkaka Managarta

A Wannan Bahasi Mai Take (Hujjojin Yin Mauludi) na ke so in kawo kadan

daga cikin dalilan yin Mauludi, amma kafin nan zan so in fara da kawo dalilan da wadanda ba .sa yin Mauludin suke kafawa, na rashin inganci ko ma haramcin yin Mauludin a gurinsu

Da farko dai su wadanda ba sa yin Maududi dinsuna kafa hujjar haramcin yin Maulud ne-1 saboda dogaro da Hadisin da Manzo (s.a.w) yake cewa: قَالَ رَسُولُ اللَّهِ - صلى الله عليه وسلم - « مَنْ أَحْدَثَ فِى  أَمْرِنَا هَذَا مَا لَيْسَ فِيهِ فَهُوَ رَدٌّ . صحيح البخاري . ج ,7, ص 36, .

Manzo (s.a.w) ya ce: Duk wanda ya fari wani abu a cikin Al-Amarinmu wanda baya ciki Addini .to an mayar masa. Sahihul Bukhari, jiz'I na 7, shafi na36

Kuma Mauludi Musamman da irin wannan launi da muke iya gani a yanzu daga baya ne aka .  irqira, don haka an mayarwa masu yin Mauludi Abunsu

Suna ganin Mauludi Bidi'a ce, alhali a Hadisi da Manzo (s.a.w) na cewa-2: وقوله صلى الله عليه و سلم : " كل بدعة ضلالة وكل  ضلالة في النار . موطأ الإمام مالك . ج .1,ص 355, .

Fadin manzo (s.a.w) Dukkan wata bidi'a-Abinda aka qirqiro- 6ata ce kuma dukkan wata 6ata .tana cikin wuta. Muwatta na Imam Malik, juz'I na 1, shafi na 355

Kuma mauludi qirqirarren abu ne, don haka makomarsa wuta. 3-Masu cewa son Annbi (s.a.w) ne ta sa suke yin Mauludi, shin sun fi Sahabbai Irinsu Abubakar, da

Umar, da Usman, da Aliyu, son Annabi (s.a.w) ne? gashi su ba su yi Mauludi ba, don haka inda .Mauludi Addini ne da su magabata su zasu fara yi

?Yadda za a gane Mauludi baya cikin Addini shi ne: meye Farillai ko Mustahabban Mauludi-4

.Ana chakuduwa maza da mata a gun mauludi, alhali yin hakan haram ne -5

Masu yin biki da murna a ranar Mauludi suna murana ne da rasuwar manzo (s.a.w) saboda a-6 .ranar da aka haife shi a ranar ya yi wafati

ke e wani Wata da wani Rana don yin Mauludin Annabi (s.a.w) Ta aita son da ake masa ne,-7 .(don Yakamata ne kullun mutum yana son Annabi (s.a.w

?Anfi Qasar Saudiyya ce son Annabi (s.a.w) meyasa su basu yin Mauludi-8

Magata-Salafus Salihin- Irinsu Shaikhul Islam Ibni Taimiyya Wa anda sun fi mu sanin Addini-9 .amma suma ba su yi ba

kwaikwayon Nasara ne da suke murna da haihuwan Annabi Isa (a.s). Idan Allah ya Yarda-10 .zamu yi Bahasi akan Wa annan Abubuwa 10 aya Bayan aya, sai a Biyomu

A ci gaba da Wannan Bahasi Mai take(Hujjojin yin Mauludi) na ke so in bijiro da Dalilan da Masu qin yin Mauludin 'Daya bayan 'Daya Wanda suka Dogara da su, sai in bada Amsoshinsu :dai dai bakin Gwargwado

Da farko suna kafa Hujjar Haramcin yin Maulud ne bisa Dogaro da Hadisin da Manzo (s.a.w)-1 ke cewa: قَالَ رَسُولُ اللَّهِ - صلى الله عليه وسلم - » مَنْ أَحْدَثَ فِى أَمْرِنَا هَذَا مَا لَيْسَ فِيهِ فَهُوَ رَدٌّ . صحيح البخاري . ج ,7, ص 36, .

Manzo (s.a.w) ya ce: Duk wanda ya fari wani abu a cikin Al-Amarinmu wanda baya ciki –Addin-to an mayar masa. Sahihul Bukhari, jiz’I na 7, shafi na36. Kuma Mauludi musamman da irin wannan launi da muke gani a yanzu daga baya ne aka qirqira, don haka an mayarwa .masu yin Mauludi abunsu

Amsa: Muna buqata zuwa ga Bayanin Ma'anar Wannan Hadisin a Wurin Masana Hadisi, kafin :mu gina Hukunci a kai, Ga bayanin kamar Haka

وقال: الحافظ ابن حجر في الفتح : وَهَذَا الْحَدِيثُ مَعْدُودٌ مِنْ أُصُولِ الْإِسْلَامِ، وَقَاعِدَةٌ مِنْ قَوَاعِدِهِ، فَإِنَّ مَعْنَاهُ : مَنْ اخْتَرَعَ مِنْ الدِّينِ مَا لَا يَشْهَدُ لَهُ أَصْلٌ مِنْ أُصُولِهِ فَلَا يُلْتَفَتُ إِلَيْهِ.

Fassara: Ibni Hajar a cikin Fatahul Bari ya ce: Wannan Hadisin ana Qirga shi daga cikin Asullan (Tushen) Addinin Musulumci, kuma Qa'ida daga cikin Qa'idojinsa, kuma Ma'anarsa shi ne: "Duk

Wanda Ya Qirqiri Wani Abu a Addini Wanda ba'a sami Asali daga cikin Addini ya Shaide shi ba .to ba'a kula da shi

.Kenan Idan Asali ko Tushen Addini ya Shaidi Abu to za'a kula da shi a Addini

:To Meye Maulud ke Qumshe da shi? Zamu Saurari Amsa daga Bakin Shaikhul Islam

قال ابن تيمية : *وكذلك ما يحدثه بعض الناس إما مضاهاة للنصارى في ميلاد عيسى عليه السلام وإما محبة للنبي صلى الله عليه وسلم وتعظيما له والله قد يثيبهم على هذه المحبة والاجتهاد لا على البدع*

أحمد بن عبد الحليم بن تيمية الحراني أبو العباس )728(، اقتضاء الصراط المستقيم مخالفة أصحاب الجحيم ، ج 1 ص 294 ,دار النشر, مطبعة السنة المحمدية - القاهرة - 1369 ، الطبعة الثانية ، تحقيق محمد حامد الفقي.

:Fassara

Ibni Taimiyya ya ce: Haka Abin da Wasu Mutane suke Qirqira ko dai sabo da Kwaikwayon Nasara ne akan Haihuwan Annabi Isa (a.s) ko dai Soyayya ne ga Annabi (s.a.w) da kuma Girmama shi, kuma Allah zai iya basu ladan Wannan Soyayyan da Qoqarin da Suka yi, ba saboda Bidi'ar da suka yi ba. Iqtidaa'u Siratil Mustaqim Mukhalsfatu Ashabul Jahim, Vol 1 P ........294

Na Tabbata inda za'a Tambayi dukkan masu yin Maulud cewa: don me kuke yin Maulud zasu :ce

.(Don Soyayyarsu ne ga Ma'aiki (s.a.w"-1

.Don Girmama Ma'aiki ya sa suke Mauludi-2

.Wanda Shekh Ibni Taimiyya ya ce: zasu iya samun lada akan haka

Tambaya anan shi ne Ashe Asal ko tushen Addini ba su Shaidi SON ANNABI ko GIRMAMA ?SHI ba

Idan Amsar shi ne: E, sun Shaida to Abinda ake buqata ya Tabbata, idan Amsar ita ce: a'a. Idan kuna biye da mu Bayan Mun kawo Bayanin Ma'anar Hadisin da Ibni Jajar ya yi Wanda ke nuna cewa: Ana nufin ne Wanda ya Qirqiro Wani Abin da babu Asul wani Ginshiqin Addini da ya ya bada Shaida a kansa to Wannan Abin ba'a kula da shi a Addini. Sai kuma Muka kawo Zancen Ibni Taimiyya akan batun bada Masu yin Mauludi lada akan Soyayyarsu ga Manzo da Girmama shi, Sai a qarshe muka yi Al-kawarin Tabbatar da cewa Addinin Musulunci ya Gina

:Mutane bisa

.Soyayyan Manzon Allah -1

.Da Girmama shi -2

:Ga Kadan daga Wuraren, Allah yana cewa

﴿...وَمَن يُعَظِّمْ شَعَائِرَ اللَّهِ فَإِنَّهَا مِن تَقْوَى الْقُلُوبِ﴾

(Wanda ya Girmama Alamu na Allah na daga cikin Taqawar Zuciya...)

Bana tsammanin da akwai mai Shakkan kasantuwar Manzon Allah Babba Alama na Allah. A :Wani Wuri kuma Allah ya sake cewa

إِنَّآ أَرْسَلْنَــكَ شَهِدًا وَمُبَشِّرًا ...لِتُؤْمِنُوا بِاللَّهِ وَرَسُولِهِ وَتُعَزِّرُوهُ وَتُوَقِّرُوهُ وَتُسَبِّحُوهُ بُكْرَةً وَأَصِيلًا((٩

Lallai Mun Turoka a Matsayin Mai Shaida Mai Bushara (8) Don Ku yi Imani da Allah da Manzonsa, kuma Ku Taimake shi, kuma Ku Girmama shi, kuma Ku Tsarkake shi Safiya da .(Maraice (9

:Akan Soyayyar Manzon Allah kuma Allah yana cewa

﴿قُلْ إِنْ كَانَ آبَاؤُكُمْ وَأَبْنَاؤُكُمْ وَإِخْوَانُكُمْ وَأَزْوَاجُكُمْ وَعَشِيرَتُكُمْ وَأَمْوَالٌ اقْتَرَفْتُمُوهَا وَتِجَارَةٌ تَخْشَوْنَ كَسَادَهَا وَمَسَاكِنُ تَرْضَوْنَهَا أَحَبَّ إِلَيْكُمْ مِنَ اللَّهِ وَرَسُولِهِ وَجِهَادٍ فِي سَبِيلِهِ فَتَرَبَّصُوا حَتَّى يَأْتِيَ اللَّهُ بِأَمْرِهِ وَاللَّهُ لَا يَهْدِي الْقَوْمَ الْفَاسِقِينَ ( 24 ﴾

Ka ce: idan ya kasance: Iyayenku, da 'Ya'yanku, da 'Yan Uwanku, da Matanku, da Danginku, da) Dukiyoyin da kuka Tara, da Kasuwancin da kuke tsoron Hasaransa, da Wuraren Zaman da kuka yarda da su, kun fi Sonsu akan Allah, da Manzonsa da Jahadi a Tafarkinsa, to Ku zauna Har sai .Allah ya zo da Al'amarinsa, kuma Allah bai Shiryar da Mutane Fasiqai

Kenan Dolenka kafi Son Allah da Manzonsa da Jahadi Sama da Iyayenka da 'Ya'yanka da 'Yan Uwanka da Matanka da Danginka da Dukiyarka da Tijaranka da Gidajenka, in ba haka ba kana cikin Fasiqi! Don haka Musulumci yana kiran Mutane ne akan Girmama Manzo da Soyayyarsa, .kuma su ne Abubuwan da Ibni Taimiyya ya ce Masu Maulidi za'a iya basu lada akan aikatasu

:Suna ganin Mauludi Bidi’a ce, kuma Ga shi ya zo a Hadisi Manzo (s.a.w) yana cewa-2

وقوله صلى الله عليه و سلم : " كل بدعة ضلالة وكل ضلالة في النار .

موطأ الإمام مالك . ج .1,ص . ,355

Fa  in Manzo (s.a.w) Dukkan wata Bidi'a  ata ce kuma dukkan wata  ata tana cikin wuta. .Muwa  a na Imam Malik, juz’I na 1, shafi na 355

.Kuma Mauludi Bidi'a ce, don haka Makomarta wuta

Amsa:  Da Farko zamu so Mu yi Ta'arifin Bidi'a a Yare da Shari'a, a yare idan aka ce Bidi'a ana :nufin

البدعة في اللغة : تطلق على الشيء المخترع على غير مثال سابق فمن أتى بأمرلم يُسبق إليه فهو مبتدع.

Bidi'a a Yare: ana  ora ta ne akan Abin da aka Qirqira ba akan Abin da ya Gabata ba, Wanda ya yi Wani Al-amari Wanda ba Wanda ya Riga shi za'a kira shi Wanda ya Qirqira

:Amma Bidi'a a Shari'a ita ce

وفي الاصطلاح : « ما أحدث مما لا أصل له في الشريعة يدل عليه.

A Shari'a ita ce: "Abinda aka Fare shi daga cikin Abubuwan da bai da Asali a Shari'a Wanda zai ."yi nuni a kan shi

Mun ji Yadda Ma'anar Bidi'a take a Yare da Shari'a, kuma Zamu yi Amfani ne da Ma'anar Bidi'a .a Shari'a ba a Yare ba, Saboda Shari'a ce aka Kallafa Mana binta ba Yare ba

To Abin Tambaya a nan shi ne: Shin Soyayyar Manzo (s.a.w) ne bai da Asali a Addini ko ?Girmama shi

Idan Har Soyayyan Manzo (s.a.w) da Girmama shi suna da Asali a Addini, kuma in dai Har

Shari'a ta yi nuni da su, to baza a kira Mauludi da Bidi'a ba, Sabda Muna Yin Maulidi ne Don: .Soyayya da Girmama Manzon Allah (s.a.w) da Muke yi

Masu cewa son Annbi (s.a.w) ne ya sa suke yin Mauludi, shin sun fi Sahabbai Irinsu-3 Abubakar, da Umar, da Usman, da Aliyu, son Annabi (s.a.w) ne? gashi su ba su yi Mauludi ba, .don haka inda Mauludi Addini ne da su magabata su zasu fara yi

Amsa: Idan Muka yi La'akari da Abinda ke umshe a cikin Maulud na Soyayyar Manzo da Girmama shi zamu iya cewa Sahabbai Sun yi irin Nasu Maudin, Wanda ta yiwu ya Sa a da irin namu Mauludin Sakamakon Sa anin Mutane da lokaci, Misali akan haka Shi ne: kowa ya San Sahabbai sun koyi karatun Al- ur'ani Amma tayiwu Hanyar da suka koya ya Sa a da namu Hanyar koyon karatun Al- ur'ani a yau, a da ana Rubuta Al- ur'ani ne a Jikin Ganyen bishiya da Fata da Ice, Amma Mu a Yanzu namu Al- ur'anin an Rubuta shi ne a Takarda, Sannan a jikin Al- ur'anin da ke Hannun Sahabbai ba igo ba Wasali, Amma a namu Al- ur'anin a kwai igo da Wasali, Sannan Tayiwu ma ta Hanyar Kaset muke koyon karatun Al- ur'ani Amma su a Zamaninsu ba Radiyo ba Kaset balle su ko yi karatun Al- ur'ani ta Hanyarsa, Amma idan aka ta shi Bayani za'a ce da kai da su duk kun koyi karatun Al- ur'ani dukda kun Sa a a Usulubin .koyon

Misali na Biyu shi ne: a Zamanin Manzon Allah Sahabbai Sun yi Neman Aure Amma Tayiwu .yanayin Neman ya Sa a da namu Neman Sakamakon Canjin Zamani da Al-ada

Sannan kowa ya San a Zamanin Sahabbai sun yi Sujada ne a kan Qasa da Dutsi da Ganye, :Amma yanzu zaka ga Mutane suna Sujada ne akan

Kafet, Tabarma, Siminti, Kwalta da sauransu, ba tare da Mutum yana jin ya Saba ma Annabi da Sahabbai ba, su masu Tuhumarmu akan yin Maulud so sukeyi su ce: Idan Annabi da Sahabbai ba su yi Abu ba ya Haramta mu yi, Muma sai mu Tambayesu cewa: Me ya Sa Ba ku Sujada akan Abin da Annabi da Sahabbai suka yi a kai? A she kuma kun Aikata Haram kuma Baku da ?Sallah

Sannan da Zaka yi Tambayi cewa: Shin Annabi (s.a.w) ya kasance yana lizimtan Al- ur'ani a Watan Azumi kamar yadda mu ke yi? Za ka ji Har da Wadanda basu yin Mauludi sun ce: E, Tayiwu ma har su kafa Hujja da Hadisin ya nuna cewa: Mala'ika Jibril ya kasance yana Sauka suna Karatu tare da Manzon Allah kullun, Amma inda zaka yi Tambaya cewa: Shin yadda Yanzu Muke yi haka suka yi? Wato An sami Mai Jan Baqi da Mai Fassarawa da Masu Sauraro a Zamanin Manzo (s.a.w)? Amsar itce a'a, to Meyasa? Tayiwu saboda wasu dalilai na Daban,

Wanda baza su Wuce cewa: Muna Ganin yin Tafsirin Al-qur'ani ga Mutane a cikin Watan Ramadan a Yanzu shi ya fi, to Amma shin mun fi Manzon Allah da Jibril sanin Abin da ya fi dacewa ne? Mun barwa Masu Tambayar mu cewa: Shin Mun fi Sabbai Son Manzon Allah ne Meyasa basu yi Maulud ba? su Amsa Wannan Tambayar cewa: shin kun fi Manzon Allah da Jibril sanin Abin da ya fi dacewa ne kuke Tafsirin Al-qur'ani a Watan Ramadan Al-hali Manzon Allah da Jibril su Taqara su ke yi a Watan ba Tafsir ba? Mun barsu su bada Amsar Wannan .Tambayar tunda suma suna Tafsir a Watan Ramadan Sa anin Abin da Manzo da Jibril suke yi

.A biyo mu don ci gaba

.Wassalamu Alaikum wa Rahmatullahi

.Marubuci: Tahir Umar Sulaiman

Sake bibiya: Munir Muhammad Sa’id